# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na huɗu: Kura da Macijiya da Damisa da Mugun Dawa


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Kura

Mugun dawa

Tsoho mai farin gemu

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” inda muke gabatar muku da hikayoyin ƙasashen Afrika masu taimakawa wajen zaman lafiya. Su dai waɗannan hikayoyi sukan ƙunshi gaskiya, kuma a lokuta da dama sukan yaye wa mutane duhun kansu. Kuma kamar yadda kuka sani ne cewa idan mutane suna zamantakewa ta lumana, suna samun damar ci gaba. Domin irin hikayoyin da muke zaɓo muku, sun shafi yadda jama’a ne ke zaman lumana a tsakaninsu, da kuma yadda sukan fuskanci wata matsala idan ta tunkare su, da yadda za su iya magance cin amana da hassada da kuma son kai. A kowace hikayar da za mu kawo muku, za ku ji wani abu mai amfani da zai taimaka muku a yanzu ko kuma nan gaba.

Don haka sai ku ba mu aron kunnuwanku, don ku saurari wannan hikaya a kan yadda aka ladabtar da kura saboda haɗamarta. Yanzu sai ku saurari wannan hikaya mai taken “Kura da Maciji da Damisa da Mugun dawa”.

MAI BA DA LABARI:

A shekarun baya can, an samu cewa Kura da Maciji da Damisa da Mugun dawa aminan juna ne. Dukkaninsu su huɗun sun haɗu sun mallaki wata gona wadda suke nomawa. Idan lokacin cin abinci ya yi, sai kowannensu ya kama gabansa ya nemi abincin da zai ci, kuma idan ya samu yakan ci shi kaɗai ne. Sai dai kuma wannan tsari nasu bai yi ƙarko ba!

Wata rana sai Kura ta ba da sharawar cewa, ya kamata su sake tsari wanda ya fi na da. Don haka sai ta kawo wani tsari mai sauƙi, wanda sauran ukun suka amince da shi. Wannan tsari kuwa shi ne cewa, a dinga samo abincin da zai ishe su su huɗun a sati guda, idan wannan ya samo wannan satin, sai wani kuma ya samo a wani satin. Sai dai kuma da gari ya waye, sai Kura ta ƙara wani sharaɗi a kan wannan yarjejeniya da suka yi jiya cewa:

KURA:

"Duk wanda ya kasa samo abincin da zai ishi kowa, to sauran ukun fa za su taru su cinye shi."

MAI BA DA LABARI:

Ba tare da kowa ya yi tunani a kan wannan sharaɗi ba, sai sauran ukun duka suka amince da shi nan take.

To a sati na farko Maciji ne da nemo abinci. Sai ya shiga daji ya dinga saran duk dabbar da ta shige ta gabansa da haƙoransa masu dafi. Don haka bai samu wata matsala ba wajen samo abincin!

Daga nan sai Maciji ya ɗauko waɗannan namun dajin da ya kashe ya zo ya shirya abinci na musamman, yadda sai da su huɗun duka suka kasa cinyewa. A sati na biyu, Damisa ce ke da nemo abinci. Da ta tashi sai ta yi kwanton ɓauna da yammaci a inda dabbobi ke zuwa shan ruwa a gaɓar kogi. Duk wanda ya kawo kai zai sha ruwa, sai ta kashe shi. Daga nan sai ta shirya wani kaɓakin nama, cikin kowa ya yi dam har ma da ƙyar suka fita aiki washegari.

A sati na uku Kura ce ke da nemo abinci. Da dare ya yi, sai ta tashi ta tafi cikin dabara ta riƙa sace naman da dabbobi suka tara, ta dinga jawo shi zuwa cikin gona. Yawanci wannan naman da Kura ta sato daga wurin zakuna da ungulaye ruɓaɓɓu ne, har ma wari yake yi. Amma fa kuma yana da yawa. Don haka kowa sai da ya ci ya ƙoshi amma yana toshe hanci.

A sati na huɗu nemo abinci ya faɗo kan Mugun dawa. To amma sai ya lura cewa Kura fa da ta kalle shi sai ta dinga lashe bakinta. Sai tsoro ya kama shi. Ita Kura tana da tabbacin cewa wannan kututturen Mugun dawan ba zai iya kama naman daji ko ɗaya ba. Da yamma ta yi, sai Kura ta haɗu da Mugun dawa, tana cewa:

KURA:

"Allah sarki, Mugun dawa!"

MAI BA DA LABARI:

Daga nan sai ta kau da kanta tana dariyar ƙeta. Wannan halayya ta

Kura fa ta sa Mugun dawa ya sha jinin jikinsa, domin kuwa ya lura cewa...

MUGUN DAWA:

"Lalle Kura ta hango cewar haka za ta faru tun farko. Don haka ne ma ta ƙara sharaɗin nan na biyu a wannan yarjejeniyar tamu:

*Duk wanda ya kasa samo abincin da zai ishi kowa, to sauran ukun fa za su taru su cinye shi."*

MAI BA DA LABARI:

Sai Mugun dawa ya fara sintiri saboda kiɗimewa kamar mahaukaci, don dai ya tabbata ya nemo wa sauran abinci. Duk dabbar da ya yi niyyar kamawa, sai ta kuɓuce masa, saboda ba shi da zafin nama, don haka sai bai kama kome ba. Ba abin da wannan bagidajen mafarauci ya dinga yi illa gurnani:

MUGUN DAWA:

"Wallahi na riga na sare. Ni dai kam gwiwata ta yi sanyi! Yaya zan yi da raina?"

MAI BA DA LABARI:

Kwatsam, sai ya ci karo da wani tsoho mai farin gemu, yana dogara sanda a wani sarari, wanda ya yi mamakin irin wannan fafutaka da Mugun dawa yake yi:

TSOHO MAI FARIN GEMU:

"Kai ɗan'uwa, me yake damunka haka har kake kuka? Ko ba ka da lafiya ne?"

MAI BA DA LABARI:

Sai Mugun dawa ya ba shi labarin halin da yake ciki. To da yake wannan tsoho mutum ne mai sihiri, sai ya ce zai taimake shi. Daga nan sai ya ɗauki wani dutse mai ƙyalli, mai kusurwa uku, ya mika wa

Mugun dawan, sai ya ce masa:

TSOHO MAI FARIN GEMO:

"Duk lokacin da kake so ka kashe wata dabba, sai ka ɗaga wannan dutsen a gabanta ka ce:

*Ya kai wannan dutse mai sihiri, ya kai wannan dutse mai sihiri!*
*Ya kai wannan dutse mai sihiri, kama min wannan nama dajin mana.*

Idan ka yi haka, nan take dutsen zai bi umarnin da ka ba shi sau da ƙafa. Daga nan kuwa sai ka ji kamar aradu ta faɗa wa dabbar. Kawai sai dai ka ji dabbar ta faɗi ƙasa matacciya. Amma fa bayan dutsen ya yi abin da ka ce masa, to dole ne sai ka koɗa shi, idan har ba so kake ya juyo kanka ba. Amma abin da za ka ce masa shi ne:

*Ya kai wannan dutse mai sihiri, ya kai wannan dutse mai sihiri!*
*Ya kai wannan dutse mai sihiri, wallahi sihirinka ya burge ni."*

MAI BA DA LABARI:

Daga nan sai Mugun dawa ya yi wa wannan tsoho godiya, kuma bai yi wata-wata ba, sai ya jarraba amfani da irin sihirin da wannan dutse mai ƙyalli yake da shi a kan hanyarsa ta zuwa gida. To da haka Mugun dawa ya kamo namun daji da tsuntsaye masu yawa. Ta haka ya samu ya tsira da ransa. Wato dai tsohon nan abokinsa bai yi masa ƙarya ba!

A lokacin da abokan zaman Mugun dawa suka ga ɗimbin naman da ya tara a ƙofar ɗakinsa, sai suka kasa magana, ba ma dai irin Kura. Ai satin nan cur, irin shagalin da aka dinga yi da abincin da Mugun dawa ya samo, ko a gidan sarki sai haka.

Kura ta sha cewa tana son ta raka Mugun dawa zuwa cikin daji, ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba, amma shi ba ya son ta san maganar dutsen nan mai sihiri, hakan ta sa da satin ya zo ƙarshe ma sai da Kura ta fara fushi, don ta kasa gano sirrin Mugun dawa.

Bayan wasu makonni sun wuce, yanzu an sake dawowa kan Mugun dawa. Sai ya sake shiga cikin daji, ba tare da ya lura da Kura tana

biye da shi a ɓoye ba. Tana biye da shi tana sanɗa cikin ciyayi masu tsayi. Daga nan sai ta ga yadda Mugun dawa yake amfani da dutsen nan mai sihiri.

MUGUN DAWA:

*"Ya kai wannan dutse mai sihiri, ya kai wannan dutse mai sihiri! Ya kai wannan dutse mai sihiri, kama min wannan naman dajin mana."*

MAI BA DA LABARI:

A nan fa Kura ta ji irin kalaman sirrin da ake faɗa wa wannan dutsen mai sihiri ya yi aiki. Sai ta zaci sanin wannan ma ya ishe ta.
Ba tare da ta ɓata lokaci ba, sai ta yi hanzari ta koma gonarsu. Don haka, lokacin da Mugun dawa ke faɗar kalmomi da ake wa dutsen kirari da su, tuni Kura ta yi nisa.
Da gari ya waye, lokacin da abokan zamanta ke ta ƙoƙarin yin aiki a gona, ita kuwa sai Kura ta yi kwanciyarta tana nishi wai cikinta ne yake ciwo. Sai dai kuma ga dukan alamu Mugun dawa bai yarda da ita ba. Kura na barin gona sai ta nufi gidan Mugun dawa. Tana zuwa sai ta yi ta duba inda dutsen nan mai sihiri yake. Tana ganinsa sai ta sace shi.
Ba tare da ɓata lokaci ba sai ta garzaya cikin daji, ba ta tsaya ba sai da ta ci karo da wata kyakkyawar barewa tana kiwo. Daga nan sai ta ɗaga dutsen nan mai sihiri a gaban dabbar, tana faɗin kalaman sirrin da ake faɗa.

*Ya kai wannan dutse mai sihiri, ya kai wannan dutse mai sihiri! Ya kai wannan dutse mai sihiri, kama min wannan nama dajin mana.*

Tana gama faɗar kalmar ƙarshe, sai kawai wannan barewa ta faɗi ƙasa matacciya. Shi ke nan dutse mai sihiri ya gama aikinsa, yanzu Kura yake jira ta yi masa kirari.
Ya jira, ya jira, amma bai ji wata magana ta yabo ba. Don haka sai ya yi fushi ya fara ƙona hannayen kura. Ta yi ta ƙoƙarin jefar da shi

amma sai ya maƙale a hannunta, sai ma ƙara zafi yake yi. Saboda tsabar kiɗimewa, sai Kura ta fara gudu tana haɗa hanya, tana ihu:

KURA:

“Wayyo! Wayyo, ƙyale ni, dutse mai sihiri! Wayyo, don Allah!”

MAI BA DA LABARI:

Amma ina, shi wannan dutse ba abin da yake so ya ji sai kalmomin nan da tsohon nan ya gaya wa Mugun dawa. Don haka cikin Kura sai ya ɗuri ruwa.

Ihunta duk sai ya tsorata sauran dabbobi suka watsu cikin daji. Ita kuwa sai ta sake guduwa zuwa gona inda abokan zamanta su uku suke aiki. Da farko sun ɗauka cewa ihun da take na ciwon cikin da yake damunta ne. Amma sai ta ci gaba da kururwa da ƙarfi, har Mugun dawa ya lura da ƙafafuwanta na gaba kamar an manne su a wuri guda. Ganin haka sai ya gano abin da ya faru. Don haka sai ya yi murmushi ta cikin gemunsa:

MUGUN DAWA:

*Ya kai wannan dutse mai sihiri, ya kai wannan dutse mai sihiri!*
*Ya kai wannan dutse mai sihiri, wallahi sihirinka ya burge ni.*

MAI BA DA LABARI:

Nan take sai dutsen ya saki hannayen kura, ya faɗo a gaban Mugun dawa. Sai ya ɗauke shi ba tare da jin tsoron zai ƙona shi ba. Ya ɗauka ne a gaban Maciji wanda ke cike da tsoro, da kuma Damisa wadda ko gezau ba ta yi ba, da kuma Kura wadda tuni cikinta ya riga ya ɗuri ruwa.

To fa tun daga wannan rana, kowace dabba ke ganin girman Mugun dawa. Bayan haka kuma, sai aka saka shi a cikin majalisar dabbobi masu hikima, inda yakan bayar da shawarwari masu amfani.

MAI GABATARWA:

To masu saurare, yanzu mun dawo gare ku. Shin ku ma kuna da wani dutse mai sihiri, ko wata baiwa da kuka ɓoye a ƙarƙashin shimfiɗunku? Ko kuma ma dai wani abu da kuke ɗauke da shi a aljihunku dare da rana? Sai ku aiko mana ta adireshinmu na yanar gizo domin mu ma muna so mu ji. Adireshin dai shi ne: www.dw-world.de/Ibe.

Ibrahim Ndiaye ya rubuta wannan hikaya.